# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Ni ma ɗan Adam ne: ’Yan Afirkan da ke fama da taɓin hankali
## Kashi na tara: Canza hankali

Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Yusuf Idris
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

Duduwa: ’yar shekara 35
Talatu: ’yar shekara 30
Musa: ɗan shekara 16
Amina: ’yar shekara 19
Dije: ’yar shekara 19
John: ɗan shekara 50
Mataimakiyar shugaban ƙasa: ’yar shekara 50
John: ɗan shekara 25
Jane: ’yar shekara 25

**Mai gabatarwa:**
Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin kashi na tara a shirinmu na “Ji Ka Karu” wanda muke kawo muku a kan mutane masu taɓin hankali a nahiyar Afirka. A cikin shirin da ya gabata, kun ji yanda Mandu ya shirya taro na addu’a don a kori aljanun da suka kama Musa. Sannan John ya ziyarci tsohon oganshi Patel don ya nuna mai cewa zai iya komawa aikinshi na kashiya. Amma dai ba su ƙare da daɗi ba. Sai kuma Dije, wadda ta kai ƙawarta Amina wurin Dr. Mudi.
Ku kasance tare da mu a cikin shirin na yau mai taken “Canza hankali”. Za mu faro ne daga wajen Duduwa da ɗanta Musa inda suka kai ziyara wurin wata ƙungiya ta masu ciwo irin na Musa bayan taron addu’ar da aka shirya ba ta warkar da yaron ba. Sun sami wata mata mai suna Talatu wadda ta karɓe su.

**Fitowa ta 1: A gidan kula da yara masu fama da ciwon ƙwaƙwalwa**

**Duduwa:** Ka gani ko Musa, ashe ba kai kaɗai ba ne. Ni da ina tunanin cewa kai kaɗai ne ke da irin wannan cutar, amma kalli! Akwai mutane da yawa irinka.

**Talatu:** Sannunku da zuwa.

**Duduwa:** Yauwa, sannunki dai!

**Talatu:** Sunana Talatu. Ni ma’aikaciya sa-kai ce a nan.

**Duduwa:** Mun gode Talatu. Wannan ɗana ne Musa. Tun yaushe aka kafa wannan ƙungiyar?

**Talatu:** Kamar yadda kika gani, har yanzu komai sabo ne. Har yanzu ƙungiyar ba ta kai shekara ɗaya ba. Kuma mutane ba su da masaniya a kan yadda za su riƙa kula da masu cuta irin wannan, sannan kuma yaran da ake haihuwa da

wannan cutar kullum ƙaruwa suke yi, sai wani mai arziki wanda ba ya so a faɗi sunashi, ya gina wannan wurin don a riƙa kula da yaran. Na ji cewa shi mutum ma yana da ɗa mai irin wannan cutar da ke kama ƙwaƙwalwar yara ta mai da su kamar wawaye ko marasa hankali.

**Duduwa:** Mhm. To, kamar me yaran suke yi a nan? Wannan kamar wata makaranta ce ke nan?

**Talatu:** To akwai abubuwa da yawa da ake yi a lokaci ɗaya, amma manufanmu a nan ita ce, mu inganta harkokin rayuwarsu, kuma mu riƙa ba su ƙwarin gwiwa a kan abubuwan da suke yi.

**Duduwa:** To yaya kuke yi kuke gudanar da haka? Na yi ta gwadawa a kan ɗana Musa tun shekaru goma sha shida da suka wuce, amma ban samu nasara ba. Don Allah, mene ne sirrinku?

**Talatu:** Gaskiya ba wani sirri. Abin da muke yi kawai shi ne mu mai da hankalinmu a kan yaro ɗaya ta hanya dabam, amma kuma duk da haka muna ba su ƙwarin gwiwa su riƙa cuɗanya da junansu.

**Duduwa:** To yaya kuma kuke yi idan kuna sa su? Ina nufin su yaran? Suna yarda kuwa?

**Talatu:** Bari ki gani! ... Yara ku saurara, kowa da kowa. Muna da baƙi yau. Mu yi musu maraba, kowa ya shirya. Ɗaya, biyu, uku! *Go!*

**Duduwa:** Musa! Suna yi maka tafi ne. Suna yi maka maraba. Ka ga a nan kowa na kallonka a matsayin mutum wanda ya kamata a ƙaunace shi.

**Musa:** Mama... Mama…

**Talatu:** Yauwa Musa, zo ka ji! Zo in gabatar da kai a wajen sauran yaran.

**Mai ba da labari:**
Sai hawayen murna suka fara kwararo wa Duduwa a lokacin da ta ga Talatu ta kama hannun Musa zuwa wurin sauran yaran da su ma suke fama da irin wannan cutar da ke damunshi. A yayin da muke barin wannan mahaifiyar a cikin halin da take ciki, bari mu koma ɗakin kula da mutane a asibitin Dr. Mudi, inda Amina da Dije ke zaune kuma suna jira su ji abin da likitan zai faɗa musu bayan Dije ta faɗa mishi duk irin abubuwan da suka faru. Ku ci gaba da sauraronmu.

**Fitowa ta 2: A asibiti**

**Likita:** Amina, a halin da kike ciki kina buƙatar kulawa a kai-a kai da kuma ba ki magunguna da za ki riƙa sha. Saboda haka, ina ba da shawarar a kai ki asibitin kula da masu taɓin hankali kawai.

**Dije:** Mene!? Ba zai yiwu ba! Ba za a kai Amina gidan mahaukata ba. Ai matsalarta ba ta yi tsanani haka ba, ka ga ai ta san ni, ta san ko wace ce ita. Muryoyin da take ji ne kawai matsalar. Idan za ka iya hana ta jin waɗannan muryoyin, za ta warke.

**Likita:** Saurare ni ki ji, 'yammata! Na daɗe ina a matsayina na likita mai duba masu taɓin hankali, kuma na san yadda wannan matsalar ta ke fiye da yanda ba kya tsammani.

Saboda haka ina da dalilin da ya sa na ce ya kamata a kai ta asibitin masu taɓin hankali don a kula da ita. Ɓa don wani abu ba ne illa don a kare lafiyarta kawai, kuma da zaran ta samu sauƙi za a sallamo ta.

**Amina:** Zan iya yin magana?

**Likita:** Kwarai da gaske, ai ke ce mara lafiya. Kina da damar ki faɗi duk abin da kike so ki faɗa.

**Amina:** Ina so in je asibitin nan. In dai har zai sa in samu lafiya, to ina so in je.

**Dije:** Amma Amina! Kin san irin labarun da muka riƙa ji a aji na yadda ma'aikatan asibiti ke cika wa masu taɓin hankali magunguna har ya shafi tunaninsu?! Ki ga ba abin da suke yi illa su zauna su ƙura wa wuri ɗaya ido kawai. Kina so ke ma ki ƙare a haka ne?

**Likita:** Dakata, dakata! Kar mu ba mara lafiyarmu tsoro da labaru masu ta da hankali!

**Amina:** Ni ina so in samu lafiya ne kawai. Ina so in ci gaba da tafiyar da rayuwa ta kamar da, in ci gaba da karatuna da…

**Likita:** A jira! A jira tukuna! … A'a, wasu dai ba sa ganewa, wallahi! … Ina zuwa, na ce a jira sai …

**Mataimakiyar shugaban ƙasa:** Dr. Mudi?

**Likita:** A'a'a, ranki ya daɗe! Ki yi haƙuri, ai ban san cewa ke ba ce. Me ya kawo ki? Don Allah shigo daga ciki, shigo!

**Dije:** Ranki ya daɗe, amma ba ke ce mataimakiyar shugaban ƙasa ba?

**M. shugaba:** Kwarai da gaske, ni ce. Amma wannan zuwan ba na aiki ba ne, saboda haka zan roƙe ki da kada ki faɗa wa kowa. Ba zan so in ji cewa kowa, musamman ma 'yan jaridu, sun ji cewa na zo ganin likita mai duba ƙwaƙwalwa ba.

**Likita:** Shi ke nan 'yammata, ku ɗan ba mu wuri. Kuma ku yi tunani a kan abin da na ce. Amina na buƙatar a kai ta asibitin masu taɓin hankali, kuma gwamma a hanzarta a kai ta. Ni da kaina zan riƙa zuwa ina duba ta a can. Saboda haka kada ku damu. Komai zai zama daidai in Allah ya yarda. Na gode. Sai na gan ku.

**Dije da Amina:** Mun gode, Likita!

**Likita:** To madalla. Yauwa!

**M. shugaba:** Na gode da damar da ka ba ni na ganinka. Na san cewa kai kaɗai ne kawai likita mai duba masu taɓin hankali a ƙasar nan, kuma na san abubuwa na yi maka yawa.

**Likita:** Kwarai, wannan haka yake. Sau da yawa na yi ƙoƙarin ma'aikatar lafiya ta ɗauki nauyin masu koyon zama likita a bangaren taɓin hankali, amma abin ya faskara. Amma dai na san ba kin zo wurina ne don ki ji yadda masu taɓin hankali suke a ƙasar nan ba.

**M. shugaba:** Ba sai na bincika ba. Ni kaina na san yadda abin yake kamar kai. Na zo ne saboda ɗana. Matsalarshi sai ƙaruwa take yi, kuma ban san matakin da zan ƙara ɗauka ba.

**Likita:** Ok, wannan ba komai. Ya kamata in gan shi. Yanzu bari in bi ki.

**M. shugaba:** Ina tunanin cewa ya samu lafiya, ya ma daina yin waɗannan maganganun da ba mai fahimta. Amma kuma kawai sai ya koma yana yadda yake yi kafin mu kawo shi wurinka.

**Likita:** Ai kula da yaro mai ciwon ƙwaƙwalwa yana da wahala gaske, kuma yana ɗaukar dogon lokaci.

**M. shugaba:** Dakata, ni ba sai ka ƙara yi min wannan bayanin ba. Abin da nake so in sani a nan shi ne, in za ka iya taimakonshi yanzun nan, kuma ba tare da kowa ya sani ba.

**Likita:** Ina da shawara mai kyau da zan ba ki: Me zai hana ki bari duniya ta sani?

**M. shugaba:** Mene ne? Ba ka da hankali ne? Ina ganin kula da kake yi da mahaukata kai ma ya fara shafanka.

**Likita:** Ya kamata a ce mutane suna ganin irin waɗannan misalan. Ya kamata su san cewa taɓin hankali zai iya shafar ko wane ne, har ma da 'yan'uwan shugabannin da suke jagorancin wannan ƙasa tamu.

**M. shugaba:** A'a! Sam! Wannan bai taso ba. Ba zan iya yin haka ba. Na ɗaya, zai zama ƙarshen yin harka siyasata. Na biyu kuma, bai kamata ɗana da iyalaina su fuskanci wannan abin ba. Ina ganin na ɓata lokacina ne. Sai dai in tura shi ƙasar waje.

**Likita:** Ranki ya daɗe! Ya kamata dukkanmu mu fara canza halayenmu. Ya kamata a ce mun rungumi matsalolin masu taɓin hankali a cikin al'amuranmu na yau da kullum a ƙasashenmu. Ba zai yiwu a ce ko yaushe mu riƙa ɓoyewa ko jin kunya ba idan aka ce a cikin iyalanmu ko 'yan'uwanmu akwai mai taɓin hankali. Mutane na shan wahala, ɗanki na ɗaya daga cikin dubbai, in ma ba miliyoyi ba a nahiyar Afirka. Sannan daga ƙarshe gwamnati na iya yin wani abu a kan lalacewar gidajen masu taɓin hankali da muke da shi.

**M. shugaba:** Hmm… Gaskiya ban kalli al'amarin ta wannan fuskar ba. Wataƙila ma wannan ya taimake ni. Wa ya sani, ta sanadiyyar yin haka ma ina iya zama shugaban ƙasa a zaɓe mai zuwa. Shi ke nan! Hakan za mu yi!

**Mai ba da labari:**
Dr. Mudi ya yi ƙoƙarin canza wa mataimakiyar shugaban ƙasa ra'ayi. A yayin da shi da mataimakiyar shugaban ƙasar suka kama hanyarsu ta zuwa duba marasa lafiyan, shi kuma John yana bakin ƙofar gidanshi cike da murna a kan abin da ya faru yanzu-yanzun nan. Ku ci gaba da sauraro.

**Fitowa ta 3: A gidan John**

**Jane:** John! Don Allah ka yi shiru, jaririyar na barci. … A'a, a'a, ikon Allah! Ikon Allah sai kallo!

**John:** Me ya faru? In ce dai ba wani abu?

**Jane:** Waƙa fa kake yi! Wannan abu da daɗi yake! Ba zan iya tuna lokacin da na ji kana waƙa kamar haka ba. Ina ganin tun kafin ka rasa aikinka ne.

**John:** To, yanzu an mai da ni kan aikina. John ya koma aiki!

**Jane:** Mijina, ina taya ka murna! Ba ranar da ta yi min daɗi kamar wannan a rayuwata. Ba ni labari, a ina za ka yi aikin?

**Mai gabatarwa:**
Da haka kuma muka kawo ƙarshen shirin na yau. A kasance da mu a shiri na goma kuma na ƙarshe don a ji yadda shirin zai ƙare. Shin Amina za ta warke kuwa? Shi kuma Musa fa? Yanzu kuma ga shi John ya samu sabon aiki, to halin da ya samu kanshi na takaici da ƙunci ya tafi ke nan? Idan kuna son sake sauraron wannan shirin da ma wasu da suka gabata, sai ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo a dw.de/lbe. Muna kuma maraba da ku a shafinmu na Facebook. Sai mun sadu a shiri na gaba. Ku huta lafiya.